*FOR IMMEDIATE RELEASE*

**AREWA24 TANA BIKIN CIKAR SHEKARA GUDA DON SAMUN NASARARTA WAJEN YADA SHIYE-SHIRYE A HARSHEN HAUSA** **July 7, 2015** – Wannan watanne ake bikin cikar shekara guda na AREWA 24, tashar talabijin ta farko da ke yada shirye-shiryenta a harshen Hausa ta Tauraron Dan-Adam don masu magana cikin yaren Hausa a Najeriya da makwabtan kasashe. Tun farkon kaddamar da ita, AREWA 24 ta zama gagarabadau a matsayin tashar da tafi kowacce yada nagartattun shirye-shiryen talabijin a cikin harshen Hausa, yaren Afirka ta Yamma da fiye da mutane miliyan hamsin suke magana da shi a duniya. AREWA 24 zata yi wannan biki ne ta hanyar amfani da shirye-shiryenta da suka fi farin jini, wadanda za su hada da shiri na musamman ta kafofin dandalin sada zumunta da kuma tattaunawa da masu kallonmu.

AREWA 24 tana mika dunbun godiyarta ga masu kallonta a ratsin Afirka ta Yamma da sauran duniya baki daya don gagarumin goyon bayan da suka bawa tashar da kuma abin da ta sa a gaba. AREWA 24 na sane da muhimmiyar gudunmowar da abokan tafiyarta suke ba ta, masu tallace-tallace da hazikan ma'aikatanta wadanda suka zage dantsensu wajen kawo nasarar da aka cimma tun da fari.

A shekararta ta farko, bangaren samar da shirye-shirye na AREWA 24 ya samar da sababbin shirye-shirye goma sha daya, wadanda suka hada da shirin da tashar take yadawa da safe wato Gari Ya Waye da kuma kasaitaccen shirin wasan kwaikwayon nan na Dadin Kowa, wadanda aka kara yawansu da shirye-shirye na kasashen ketare da AREWA 24 ta dora murya akai ko ta dora fassara cikin harshen Hausa don fara yada shi a cikin Afirka Ta Yamma. Saka jari don kirkiro shirye-shiryen Hausa ya bawa tashar damar watsa shirye-shirye daga awa hudu a lokacin da aka kaddamar da ita zuwa awa ashirin da hudu kamar yadda take a yau, wanda ya kunshi abubuwa birjik na ilimantarwa da nishadantarwa ga dukkan iyali.

Manajan kula da shirye-shirye Rakiya Usman ta bayyana cewa, "Bikin shekara daya na AREWA 24 ya nuna yadda ake da bukatar sababbi da managartan shirye-shirye na harshen Hausa a yankin da kuma masu magana da yaren a ko ina. Wannan dandali mai karsashi da nishadantarwa na yada shirye-shirye ya samar da abubuwa cikin harshen Hausa akan Hausawa don Hausawa, sannan kuma ya bamu damar ba wai kawai bayyana al'ada da fikirar mutanenmu ba, har ma da bayyana rayuwarmu da tsarin tafiyar da ita don nunawa sauran 'yan Najeriya da makwabtansu na Nijar, Chadi da Kamaru."

Jajircewar AREWA 24 wajen samar da shirye-shirye cikin yaren Hausa na talabijin ya cike wani gibi don masu jin yaren Hausa da suka watsu a cikin duniya wadanda kuma suke ziyartar filin sada zumunta na AREWA24 ta yanar-gizo don tabbatar da karin maganar nan ta "Kowa ya bar gida, gida ya bar shi" wajen ganin al'adunsu da haduwa da al'umarsu a ko'ina fadin duniya. Akan dora shirye-shiryen da AREWA 24 suka samar a kan youtube.com/AREWA24channel duk sati, kuma tashar tana amfanar masu amfani da AREWA24.com, facebook.com/AREWA24 da kuma twitter.com/AREWA24channel.

Kano, Nigeria | The AREWA24 Channel, LLC | Lagos, Nigeria
1212 Market Street, Suite 200
San Francisco, CA 94102
*+1-415-561-4884*

Bayani Kan AREWA 24: AREWA24 (arewa24.com) ita ce tashar talabijin ta Satalayit daya tilo kuma ta farko a Arewacin Najeriya da ke yada shirye-shiryen Hausa awa 24 a rana wadda ‘yan yankin suka samar don yada shirye-shiyen kan rayuwar Arewacin Najeriya, ala’ada, mutunci, matasa, cinikayya, fasaha da kuma nishadantarwar iyali. AREWA24 tana nan a tauraron dan adam na EUTELSAT 16A, kwano na kallon sama, Frequency 10804H, SYMBOL rate 30000 kuma a rukunin tashoshin ACTV. Abokan gamayyar yada shirye-shiryen AREWA 24 sun hadar da Jodan Media City, Eutelsat da Globecast. Don Karin bayani a tuntubi: info@arewa24.com

Kano, Nigeria

The AREWA24 Channel, LLC
1212 Market Street, Suite 200
San Francisco, CA 94102
*+1-415-561-4884*

Lagos, Nigeria